## AREWA24 TA BIJIRO DA JERIN SHIRYE-SHIRYENTA A WATAN AZUMIN RAMADAN NA SHEKARAR 2017

**11 Afrilu, 2017 -** AREWA24 ta sanar jerin shirye-shiryenta a watan Ramadan na shekarar 2017. Tashar Arewa24 ita ce tashar tauraron dan adam ta yan arewa ta farko dake yada shirye-shiryenta cikin harshen hausa na tsawon sa'o'i 24 a dukkanin ranakun mako, wadanda 'yan Arewa ke shiryawa domin 'yan Arewacin Najeriya da kuma masu magana da harshen Hausa dake Nageriya da kasahen dake Makotaka da ita.

A wannan shekarar, za a fara azumin watan Ramadan a ranar 26 ga watan mayu kuma zai kai har zuwa 25 ga watan Yuni. A cigaba da kokarin shigar da shirye-shiryen azumin watan ramadan a cikin Shahararrun shirye-shiryen Arewa24, Tashar zata dinga kawo muku kayatattun shirye-shiryen azumin watan Ramadan. Wadannan kayatattun shirye shirye sun hada da "**Ababen koyi daga rayuwar Annabi (S.A.W.)"** wasu jerin shirye-shirye dake sa zurfin tunani mai tasiri a rayuwar yau da kullum da kuma; shirin **"Akushi da Rufi,"** shirin girke-girke dake nuna girke-girken gargajiya na Arewacin Najeriya. Tashar Arewa24 zata rika kawo shirye-shirye azumin watan Ramadan daga kasashen duniya a cikin jerin shirye-shiryenta na yau da kullum.

Shugabar sashen shirye-shiryen na Tashar Arewa24, Rakiya Usman ta bayyana cewa," zama a gida tare da iyali wani bangare ne daga dabi'un mutane a watan azumin Ramadan, don haka wadannan kayattatun shirye-shirye na watan azumin Ramadan an shirya su ne domin nishadaantar da iyali. Tashar Arewa24 ta bi sahun al'ummar arewacin Najeriya wajen taya su murnar wannan lokaci ta hanyar samar da shirye-shirye na musamman domin iyali,"

A karon farko a wannan shekarar, Tashar Arewa24 zata rika kirkiro shirye-shirye domin wasu daga cikin abokan huldarta dake son tallata hajarsu. Tashar Arewa24 dake gudanar da mahimman aikin shirye-shiryenta a Kano, ta samu damar kirkiro shirye-shirye a cikin harshen Hausa wadanda suka dace da al'adun Hausawa da kuma isar da mahimman sakonni.

Kari akan shirin **Ababen koyi daga rayuwar Annabi (S.A.W.)** da **Akushi da Rufi,** shirye-shiryen Tashar Arewa24 na azumin watan Ramadan na shekarar 2017 sun kuma kunshi:

- **Ramadan in the City**: Wannan shiri ne daga tashar Al-jazeera dake duba al'amuran addini da kuma ibadu wanda muslmai ke gudanar wa a yayin azumin watan Ramadan a Kasashe 31 a fadin duniya.

- **Muslim Scholars** ("Malaman Addini"): Wannan shiri na duba rayuwar Malaman Musulunci da suka fara yin bincike kan ilimin kimiyya, lissafi da kuma adabi.

- **The Glories of Islamic Art**:  Shiri ne dake nuna kayayyakin fasaha da masu fasahar zane na muslunci suka bari da kuma bayyana alakar dake tsakanin kyawawan zane-zane da kuma sakonnin Musulunci.

- **Stories of the Followers (Tabi'een):** Wannan shiri ne na yara dake bayyana tarihin magabata wadanda suka taka rawa wajen yada addinin Musulunci.

- **Stories of the Righteous  (Saliheen):** Shiri ne dake duba ga rayuwar Mutane na Kwarai, wadanda suka shahara a cikin tarhin Musulunci wadanda kuma halayensu da iliminsu da nagartarsu da kuma kyawawan dabi'unsu wadanda ke shiryarwa tare da zaburar da suke zuwa bayansu.

An samar da tashar AREWA24 a shekarar 2014 domin ta cike gibin dake akwai na samar da shirye-shirye masu nishadantarwa cikin harshen Hausa da kuma shirye-shiryen tsarin rayuwa dake nuni da abubuwan alfahari na rayuwar Arewacin Najeriya da al'adu da kade-kade, da fina-finai da fasaha da girke-girke da kuma wasanni.

A yau, Kimanin mutane milyan 80 dake magana da harshen Hausa a Najeriya da kuma yammacin Afirka na kallon AREWA24 akan tauraron dan adam na Eutelsat na kyauta da kuma akan DStv (tasha ta 261) da kuma Gotv ( Tasha ta 101) a Najeriya. Haka kuma ana iya samun dukkanin shirye shiryen Tashar AREWA24 akan shafin YouTube kyauta da kuma manhajar waya ta tashar. Shafukan sada zumunta naa tashar Arewa24 sun kirkiri wata dama ga al'umma su tattauna akan shirye-shiryen ta na harshen hausa da kuma yada manufofinta.

**Game Da Arewa24:** AREWA24 (arewa24.com) gidan talabijin din Arewacin Najeriya ne na farko a tauraron Dan-Adam mai yada shirye-shiryensa 24/7 kyauta, wanda ke gabatar da shirye-shiryensa akan rayuwar Arewacin Najeriya, alʿʿadu, matasa, kasuwanci da nishadantar da iyali. AREWA24 ta dukufa wajen habakawa da kuma cike gibin da masu magana da harshen Hausa suka rasa na shirye-shiryen Hausa a duk fadin duniya, wadanda da yawansu sukan kama tashar AREWA24 ta hanyar yanar gizo domin ganin alʿʿadarsu da kuma ta sauran mutanen duniya. Ana dora shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta kowane sati a youtube.com/AREWA24channel, kuma tashar tana karuwa da masu kallonta ko da yaushe a AREWA24.com, Facebook.com/AREWA24, Instagram.com/AREWA24channel, da twitter.com/AREWA24channel. AREWA24 tana kan EUTELSAT 16A, horizontal polarization, frequency 10804, symbol rate 30000 da kuma tauraron Dan-Adam na ACTV. Abokan huldar AREWA24 sun hada da Jordan Media City, Eutelsat da Globecast. Ana rarraba shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta a duk fadin Arewacin Najeriya tare da hadin gwiwar hukumar talabijin ta Najeriya (NTA). Tashoshin da suka fara gudanar da wannan hadakar ta NTA-AREWA24 sun hada da NTA-Abuja, NTABauchi, NTA-Kaduna, NTA-Kano, NTA-Maiduguri da NTA-Sokoto, kuma zamu ci gaba da kutsawa cikin sauran tashoshin NTA a Arewacin Najeriya gaba dayan wannan shekarar.